# DEUTSCHE WELLE
# JIKA KARU

## Cin zarafi ta hanyar lalata tsakanin al’umma a Afirka
## Kashi na goma: Wannan shi ne labarina


| | |
|---|---|
| Wanda ya rubuta: | Chrispin Mwakideu |
| Wanda ya fassara: | Yusuf Idris |
| Wadda ta tace: | Halima C. Schmaling |


**’Yan Wasa:**

| | |
|---|---|
| Fati: | ’yar shekara 16 |
| Gambo: | ɗan shekara 18 |
| Julie: | ’yar shekara 40 |
| Hadiza: | ’yar shekara 30 |
| Dauda: | ɗan shekara 40 |
| Adams: | ɗan shekara 12 |

**Mai gabatarwa:**

Masu sauraronmu, barkanmu da sake kasancewa da ku a cikin wannan shiri na "Ji Ka Karu" kashi na goma kuma na ƙarshe a jerin shirye-shiryen da muke kawo muku a kan cin zarafin mutane a nahiyar Afirka**.** A cikin shiryin da ya gabata kun ji cewa an damƙe shugaban 'yan ta'addan nan waɗanda suka gallabi mutane wajen yi wa mata fyaɗe, da yadda Hadiza ma ta faɗa tarkonsu. Yanzu yaya labarin zai ƙare? Sai ku biyo mu cikin wannan shiri mai taken "Wannan shi ne labarina".

Za mu faro ne daga makarantar su Fati, inda ta fara ci gaba da zuwa gudu da safe kafin ta je aji. Da ma kuma Gambo, ɗan makarantarsu kuma zakaran wasannin motsa jiki na makarantar, na neman wannan damar.

**Fitowa ta 1: A filin wasa na makarantar**

**Gambo:** An gai da Fati!

**Fati:** Woooi…! Ka daina ba ni tsoro haka! Me kake nema da ni ne?

**Gambo:** Me nake nema da ke? Ka ji wata irin tambaya. ta shirme.

**Fati:** Ban sani ba. Wataƙila sabuwar wayar da ta fito.

**Gambo:** Akwai ki da ban dariya wallahi, Fati! Ji mana, me zai hana mu ɗan yi gudu tare zuwa cikin dajin can? Na san wani wuri mai kyau da za mu...

**Fati:** A'a! Ba na jin yin gudu da kowa. Yau ni ɗaya nake so in yi gudu. Don Allah kar ka zo kusa da ni.

**Gambo:** Haba 'yammata, kwantar da hankalinki, ba zan ji miki ciwo ba.

**Fati:** Kar ka zo kusa da ni! In ba haka ba zan yi maka ihu. Ina gargaɗinka. Ka ƙyale ni! In ba haka ba zan yi ihu. A'a, kar ka taɓa ni mana! Wayyo Allah! A taimake ni, wayyo Allah!

**Gambo:** Ji mana! Kai! Yarinyar nan fa ba ta da hankali. Kwata-kwata ba ta da hankali. Me na yi mata? Kafaɗarta fa kawai na taɓa. Me ya sa take ce da gudu haka? Ikon Allah!

**Mai ba da labari:**
Ba hauka Fati ta yi ba, kuma ta nuna wa Gambo cewa kar ya kuskura ya matso kusa da ita. Fati na ƙoƙarin farfaɗowa ne daga fargabar da ta shiga wanda ya nuna cewa ta fi tsorata fiye da lokacin da Gambo ya zo wurinta a karin farko. Irin halin da malaminta ya sa ta a ciki bai gushe daga zuciyarta ba ko kaɗan. Julie na taimaka wa Fati wajen ganin cewa ta manta da abin da ya same ta, kuma ta ɗauki mata kan kare kanta daga faruwar wani abu makamancin wannan. Idan har ta gane cewa tana fuskantar wata barazana, to lalle sai Fati ta yi nesa daga wurin ba tare da wani ɓata lokaci ba. Saboda haka sai ta yi ta gudu. Ta yi ta gudu, nesa daga wajen Gambo, nesa daga makarantar, nesa daga komai. Kafin ta san abin dake faruwa, sai kawai ta tsinci kanta a gaban cibiyar da Julie take, tana haki, kuma tana tunanin yaya aka yi har ta kawo nan. Tazarar kilomita goma ce tsakanin makarantarsu da wurin! A cikin cibiyar, Julie na gefe ɗaya tare da Hadiza inda take ba ta shawarwari.

**Fitowa ta 2: A cibiyar Julie**

**Julie:** Hadiza, ina so in nuna matuƙar farin ciki da yadda kika dage na sha'awar zuwa karɓar shawarwari. Kin can cewa wannan shi ne siratsi mafi wahala a ƙetarar rayuwarki. Yana iya ɗaukar wasu shekaru da dama kafin ki kawo inda

kike yanzu, wasu ma ba sa kaiwa ko'ina.

**Hadiza:** Na gode Julie. Ai gaskiya ƙoƙarinki ne ya sa ni hakan. Kin san cewa lokacin da na zo nan, na riga na fara tunanin kashe kaina bayan abubuwan da suka faru da ni. Hatta mijina Dauda shi ma ya guje ni. Ke kika ba ni ƙarfin gwiwar ci gaba da rayuwata. Sannan kuma na ga cewa ashe ba ni kaɗai ba ce irin wannan abin ya faru da ita, muka koma wata ƙungiya na taimaka wa juna. Ya taimaka min sosai. Ya nuna cewa ba ni kaɗai ba ce a irin wannan halin.

**Julie:** To Hadiza, yaya kike ji dangane da maganar taron da za mu yi? Kin ƙara yin tunani a kan yin magana da faɗan labarinki?

**Hadiza:** E, na yi, kuma na tabbatar da cewa ina so in yi. Ina jin cewa yanzu zuciyata ta yi ƙarfin da zan iya magana don in taimaka wa wasu matan da su ma irin abin da ya faru da ni ya faru da su. Ina so jama'a su ji labarina.

**Julie:** Fati! Me ya faru? Wani abu ya same ki ne?

**Fati:** E, na gudu ne kamar yadda kika faɗa min. Na yi ta gudu ne har na kawo nan. Na fuskanci wata barazana ce, kuma kin ce mu gudu. Yanzu kuma sai na fara tunanin cewa wataƙila ma ɗan makarantarmu yana so ne kawai ya gayyace ni hira. Amma ba zan iya ba, ba yanzu ba tukuna.

**Julie:** Kar ki damu! Komai zai tafi daidai.

**Hadiza:** Zo ki zauna, na kusa gamawa, bari in kawo miki ruwa ki sha, kin gaji sosai.

**Fati:** Kwarai na gaji, ruwan zai taimaka min. Na gode ƙwarai da gaske, Hadiza.

**Julie:** To yanzu Fati, faɗa min me ya faru.

**Fati:** Akwai wani yaro ne, sunanshi Gambo. Da farko sai ya ce in bi shi mu shiga daji, sai kuma ya fara matsowa kusa da ni, yana matsowa, ni kuma sai na fara wani irin tunani. Da kuma ya miƙo hannu zai taɓa ni, sai na ji kamar zan yi amai, sai na … sai na tsorata, sai na gudu. Na yi ta gudu kawai. Ban ma san inda nake zuwa ba sai dai na tsinci kaina a nan.

**Julie:** Kin birge ni, Fati. Kuma na ji daɗi da kika zo nan.

**Fati:** Julie, idan na faɗi labarina a wurin taron ranar Asabar, kina ganin zai iya taimaka wa waɗansu 'yammatan? Ki na ganin zai taimaki wasu 'yammatan da suka samu kansu a cikin irin halin da na samu kaina?

**Julie:** Fati, na tabbata zai taimaka. Ya kamata su san cewa kamar yadda kika sani, abin da ya faru da su ba laifinsu ba ne, cewar ya kamata su fito su faɗa, kuma su samu taimako! Amma kuma sai in kin yarda, ba wanda zai sa ki dole. Ke kaɗai kika san cewa ko kin shirya ki faɗi labarinki.

**Mai ba da labari:**
A yayin da Fati da Julie ke magana, ita kuma Hadiza ta fita don ta kawo wa Fati ruwan sha. Ashe ba ta san cewa mijinta Dauda yana kan hanyarsa zuwa cibiyar ba. Ashe yana ta neman Hadiza makwanni da suka wuce, bayan ya koma ƙauyensu bai same ta a gida ba. Daga baya sai ya tuna abin da ya faɗa mata dangane da cibiyar Julie da ƙungiyar tata.

**Dauda:** Hadiza!

**Hadiza:** Kai!

**Dauda:** Hadiza, ki yi haƙuri. Ba na yi niyyar in tsorata ki ba ne.

**Hadiza:** Me kake nema, Dauda?

**Dauda:** Ko muna iya zama wuri guda don mu yi magana?

**Hadiza:** Ina! Akwai… ba wani wuri ko lokaci! Me ma kake nema a wurina tukuna? Ka guje ni! Ka ce kana fuskantar wahala saboda kana zama da ni, kuma kai kana so ka ci gaba da rayuwarka kamar da. To ka ci gaban?

**Dauda:** Hadiza, me zan ce_ Na zama sakarai ne. Na tafi ne saboda an yi miki fyaɗe, sannan kuma jama'a suka fara guduna. Kowa sai gudunmu yake yi bayan mummunan abin da ya faru, ni kuma sai … sai na kasa daurewa. Ya ɗauke ni ɗan lokaci kafin na gane cewa ba zan iya rayuwa ba sai da ke. Ba wani abu da zan iya yi matuƙar ba kya nan.

**Hadiza:** Haka ne? Dauda, ka guje ni a lokacin da nake matuƙar buƙatar taimakonka. Ina matuƙar buƙatarka, amma ka guje ni!

**Dauda:** Hadiza, don Allah, ina roƙon ki. Ki yi haƙuri, ki yafe min! Al'amarin ne ya taɓa ni sosai, musamman rasa 'yarmu da muka yi, lokacin da kika yi ɓari bisa dalilin fyaɗen nan. Amma don Allah ki yafe min, ki dawo!

**Hadiza:** To a gaskiya zai ɗauki lokaci. Ba zan iya yanke shawarar

wani irin wannan ba a lokaci ɗaya. Sannan akwai wani abin da ya kamata ka sani. Julie ta shirya wani taro ranar Asabar ɗin nan, don ta faɗakar da jama'a a kan cin zarafin mata da ya yi yawa, kuma ta tursasa wa gwamnati a kan ta ƙara fitar da wasu ƙwararan dokoki na hukunta waɗanda suka aikata wannan laifin na yin fyaɗe. Na yarda cewa zan yi magana a lokacin taron.

**Dauda:** To, me za ki ce?

**Hadiza:** Zan ba da labarina ne.

**Dauda:** A'a! A'a Hadiza, kar ki yi haka! Kin san fa abin da yin haka yake nufi kuwa? Yana nufin cewa fa jama'ar ƙasar nan gaba ɗaya za su san abin da ya faru da ke! A'a, Hadiza! Kar ki ki haka.

**Hadiza:** To, ai da ma abin da muke so ke nan.

**Mai ba da labari**:
To bayan 'yan kwanaki kaɗan, sai aka gudanar da babban taron da ƙungiyar Julie mai yaƙi da cin zarafin mutane ta shirya. Jama'a da dama sun halarci taro, musamman ma bayan an damƙe shugaban ƙungiyar nan mai cin zarafi da kai wa mutane farmaki. Ɗakin taron ya cika maƙil da manyan jami'an gwamnati, 'yan jarida, da jama'ar gari. Farin ciki a wurin Julie sai wanda ya gani.

**Fitowa ta 3: Taron yaƙi da cin zarafin mutane**

**Julie:** Jama'a, ku saurara, jama'a, ku saurara! Kamar yadda za ku ji, ba mata ne kawai ake cin zarafinsu ba. Za ku ji labari

daga bakin wani ɗan karamin yaro, da wata yarinya matashiya, da ma wata matar aure da wasu 'yan ta'adda suka yi wa fyaɗe, da dai sauransu. Waɗannan su ne labarunsu. Mai ba da labarinshi na farko wani ɗan ƙaramin yaro ne da na haɗu da shi kwanan nan. Ya rubuta labarinsa ne, kuma zai karanto mana domin mu ji. Jama'a, a tafa wa Adams!

**Adams:** Ni sunana Adams. Yau na cika shekaru goma sha ɗaya, kuma ga labarina…

**Mai gabatarwa:**

Ɗaya bayan ɗaya, waɗanda suka sha da ƙyar daga cin zarafi, ko muzantawa, ko fyaɗe, su ka yi ta ba da labarinsu. Duk wanɗada suke zaune a ɗakin taron sai da hankalinsu ya tashi. Daga ƙarshe sai gwamnati ta gane muhimmancin buƙatuwar samar da dokar da za ta kare matasa, da kuma samar da doka mai tsanani ga waɗanda suka aikata laifuffukan da suka jiɓanci cin zarafi da aikata fyaɗe. Daga ƙarshe dai an fara sa ran cewa akwai mafita.

Da haka kuma muka kawo ƙarshen wannan shiri wanda shi ne na ƙarshe a cikin jerin shirye-shiryenmu a kan cin zarafin mutane da yi wa 'ya'ya mata fyaɗe a nahiyar Afirka. Chrispin Mwakideu ya rubuta wannan shiri baki ɗayansa. Ana iya ziyartar adireshinmu na yanar gizo domin ƙara sauraron wannan shiri da ma wasu da suka gabata a dw.de/lbe. Kuma ana iya buɗe shafinmu na Facebook. Sai kuma mun ƙara saduwa a wani sabon shirin. Ku huta lafiya.

**'Yan Wasa:**

Faruk Dagtsam
Auwal Sherrif
Rukayyatu Bala
Zainab Bala
Mercy Shekari
Adam Yaro
Munir Isa
Kabiru Mohammed
Zainab Ibrahim
Maryam Mohammed
Aishatu Modibbo Wali
Maryam Bala
Ali Shehu Shagari